## SŨRATUL HUMAZA سُورَةُ الهُمَزَةِ

Tana bayãni ga hana aibanta wasu mutãne, da hana gĩba da raɗa a tsakãnin Musulmi dõmin ginin al'umma ya tabbata, wanda ya karya shi, a sanya shi wuta ta cikin ginin shikã-shikai.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Bone ya tabbata ga duk mai nune, mai zunɗe (mai raɗa)

*2.* Wanda ya tara dũkiya, kuma ya mayar da ita abar tattalinsa.

*3.* Yana zaton cẽwa dũkiyarsa za ta dawwamar da shi.

*4.* A'aha! Lalle ne zã a jẽfa shi a cikin Huɗama.

*5.* Kuma me ya sanar da kai abin da ake ce wa Huɗama?

*6.* Wutar Allah ce wadda ake hũrãwa.

*7.* Wadda take lẽƙãwa a kan zukata.

*8.* Lalle ne ita abar kullẽwa ce a kansu.

*9.* A cikin wasu ginshiƙai miƙaƙƙu.

وَيۡلٞ لِّكُلِّ هُمَزَةٖ لُّمَزَةٍ ١

ٱلَّذِي جَمَعَ مَالٗا وَعَدَّدَهُۥ ٢

يَحۡسَبُ أَنَّ مَالَهُۥٓ أَخۡلَدَهُۥ ٣

كَلَّاۖ لَيُنۢبَذَنَّ فِي ٱلۡحُطَمَةِ ٤

وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡحُطَمَةُ ٥

نَارُ ٱللَّهِ ٱلۡمُوقَدَةُ ٦

ٱلَّتِي تَطَّلِعُ عَلَى ٱلۡأَفۡـِٔدَةِ ٧

إِنَّهَا عَلَيۡهِم مُّؤۡصَدَةٞ ٨

فِي عَمَدٖ مُّمَدَّدَةِۭ ٩